# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na takwas: Har a makarantu

Wanda ya rubuta: Nkoji C. Muhoho
Wanda ya tace: Maja Braun
Wanda ya fassara: Kabir Isa Jikamshi

**'Yan wasa:**

Sama'ila: ɗan shekara 17
Hadiza: 'yar shekara 15
Adamu: ɗan shekara 36

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu", inda muke kawo muku wasan kwaiwayo dangane da kula da lafiya. A shirin da ya gabata kun ji yadda Sama'ila da ƙawarsa Hadiza suka yi wa iyayensu mata bayanin yadda za su riƙa tsaftace abincin da suke sarrafawa ko kuma ci. Daga bisani kuma, Sama'ila da Hadiza da iyayen nasu suka je asibiti domin a auna su. Yanzu bari mu samu ƙarin haske game da yadda waɗannan matasa suke ci gaba da taimakawa a makantar garinsu domin a hana yaɗuwar cutar gudawa.

**Fitowa ta 1: A makarantar sakandare**

Sama'ila, Hadiza

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Hadiza! Hadiza! Ga ni nan. |
| **HADIZA** | A'a, Sama'ila! Me kake yi a wannan sashe na makaranta? Kamata ya yi na gan ka a ɓangarinku. |
| **SAMA'ILA** | Na zo in gan ki ne, Hadiza. Kin san cewa, yanzu-yanzu na bar banɗakinmu, kuma kin san wani abu? Na damu. |
| **HADIZA** | Mene ne yake faruwa? Ina fata lafiya. Ko kuma matsalarka ta yin bayan-gidan macizai ta sake dawowa? |
| **SAMA'ILA** | Hadiza ke nan! Haba ke kuma. Yanzu, ina da ƙoshin lafiya sosai! |
| **HADIZA** | Na ji. Mene ne kuma ya faru a banɗakinku? Ni na san matsalar banɗakinmu. |
| **SAMA'ILA** | Kudaje! |
| **HADIZA** | E, akwai ƙudaje a ko'ina. Kudaje a cikin ramin masai, a jikin bango, a waje, a kan tufafinmu. Kudaje yama-yama a kusan ko'ina. Gwazarma a kan daɓen banɗakin, da kyankyasai ko'ina, da dai abubuwan ƙyama barkatai. |

**SAMA'ILA** Kuma kin san wani abu, Hadiza? Waɗannan banɗakunan, ba su da nisa sosai daga wurin da muke cin abinci.

**HADIZA** Wannan ma gaskiya ne.

**SAMA'ILA** Ina tunani game da abin da muka koya wurin Kawu Adamu game da ƙwayar cuta, da kuma gubar da suke haddasa gudawa, da ƙwayayensu da ƙudaje suke samu ta bayan-gidan jama'a.

**HADIZA** Dole mu yi wani abu.

**SAMA'ILA** Kuma dole mu hanzarta yin hakan. Na damu ƙwarai game da dukanmu a makarantar nan. Nakan yi tunanin yadda kusan ko da yaushe muke cuɗanya da irin waɗannan ƙwayoyin cuta da hatsuransu, ba tare da mun sani ba!

**HADIZA** Ni ma na damu game da iyalanmu, abokai da dukan mutanen da muke cuɗanya da su bayan an tashi daga makaranta.

**SAMA'ILA** Na damu Hadiza, ba ki sani ba. Mai yiwuwa ni ne fa na yaɗa waɗannan ƙwayoyin cutar daga banɗakinmu zuwa ƙanwata Fati.

**HADIZA** A'a! A'a, Sama'ila, don Allah ka daina irin wannan tunanin. Akwai hanyoyi masu yawa da mai yiwuwa jinjira Fati ta samu waɗannan ƙwayoyin cuta. Hanyoyi dabam-dabam, hatta daga kayan marmari da ake sayowa a kasuwa. Ba mamaki, ita ce ta harba maka ƙwayoyin cutar.

**SAMA'ILA** To! Amma kin san cewa ba zan iya daina yin wasawasin lamarin ba.

**HADIZA** Ya kamata mu yi tunanin abin da muka sa gaba. Mu manta da abin juyayin da ya wuce. Allah ya ji ƙan jinjira Fati.

**SAMA'ILA** Amin. Bari mu yi wannan domin jaririya Fati!

**HADIZA** Mene ne?

**SAMA'ILA** Mu wanke banɗakin, mashiriciya! Wannan shi ne abin da muke magana a kai. Ki same ni a kusa da ginin banɗakinku a lokacin shaƙatawar ɗalibai.

**HADIZA** Banɗakinmu?

**SAMA'ILA** E. Bari mu yi… ummm… wani nazari game da abin da ya kamata a yi, daga nan… Kash! An kaɗa ƙararawa.

**HADIZA** Sai na gan ka lokacin shaƙatawa.

**SAMA'ILA** To, shi ke nan. Sai mun haɗu a kusa da banɗakin.

**MAI BA DA LABARI**

Tirƙashi! Ga waɗannan matasa abokan juna, haɗuwa a kusa da banɗaki ba za ta zama wani abin da mutum zai yi ɗokinsa ba. Amma kuma matasan biyu sun fi damuwa ne game da ƙazantar da ke cikin banɗakin, wadda takan iya jefa jama'a cikin hatsarin kamuwa da cutar gudawa.

**Fitowa ta 2: A banɗakin makaranta**

Hadiza, Sama'ila

**HADIZA** Kai kai kai! Waɗannan ƙudajen… Kai kai kai! Wannan tamkar a ce ƙudaje sun mamaye wurin. Duba su! Ga su nan, sun yi caka-caka a ko'ina. Kai!

**SAMA'ILA** Kai! A kan daɓen ƙasa, da jikin bango, da jikin silin… Kin ga ma ga su nan a kan tufafinki.

**HADIZA** Kai kai kai! Ku tafi, ku tafi, ku kama gabanku! Waɗannan ƙudajen abin ƙyama. Ku tafi! Za ku sanya mini cutar gudawa. Ku tafi, ku tafi!

**SAMA'ILA** Hadiza ke nan. Kina magana da su kamar za su iya jinki. Mai yiwuwa za mu ɗauki matakan da za su sa su bar wurin nan. Kai!

**HADIZA** Kai! Ta yaya?

**SAMA'ILA** Ina jin ya kamata mu nemi taimako daga Kawu Adamu. Ki tuna fa, shi jami'in kiwon lafiyar jama'a ne. Zai san abin da za a yi.

**MAI BA DA LABARI**

Tabbas! Wanshekare Uncle Adamu ya raka Sama'ila da Hadiza makaranta. Shakka babu, a matsayinsa na jami'in kiwon lafiya zai yi matuƙar farin ciki ya ba da taimako iya ƙarfinsa.

**Fitowa ta 3: A banɗakin makaranta**

Adamu, Sama'ila, Hadiza

**ADAMU** Kai! Wannan wane irin wari ne haka? Kai! Na ga abin da kuke nufi. Wannan wata babbar salsalar cuta ce. To, wai ma kimanin ɗalibai nawa ne suke amfani da wannan banɗaki?

**SAMA'ILA** Ai, Kawu, kimanin ɗalibai ɗari uku daga ɓangaren makarantarmu.

**HADIZA** Akwai kuma wasu masu yawa daga tamu makarantar. … Saura kaɗan in haɗiye wani… Ku taho, mu fice daga wurin nan! Ku taho! Kai!

**SAMA'ILA** Haka ne Hadiza, warin wurin ya wuce misaltuwa. Mu wuce!

**HADIZA** Hakan ya fi. Zan iya yin magana da ku bakina buɗe!

**ADAMU** Kwarai kuwa, wancan wurin yana wari sosai. Me kuke jin zai faru, idan alal misali rabin ɗalibai suka kamu da cuta, sannan suka yaɗa ta a gidajensu? Mutane nawa ne za su iya harbuwa a cikin watanni biyu, ga misali?

**SAMA'ILA** Wai wai wai! Kai! Wannan wani bala'i ne a kwance da yake jiran lokacin da zai wakana.

**HADIZA** Haka ne. Uncle Adamu, bayan mutum ya samu ƙwayoyin cuta daga waɗannan ƙudajen, a nan take cutar za ta kama shi?

**ADAMU** A'a! Ba nan take cutar take nunawa ba. Takan ɗauki kwanaki kamar huɗu zuwa bakwai. Ya danganta ga mutum, da yanayin ƙoshin lafiyarsa, da yadda jikinsa yake bijirewa ƙwayoyin cuta, da wasu dalilan kuma dabam. Amma kuma ga yara, cikin hanzari cutar take bayyana.

**SAMAILA** Kamar dai abin da ya faru ga jaririya Fati.

**ADAMU** E, ƙwarai kuwa, kamar abin da ya faru ga jaririya Fati ke nan.

**HADIZA** Uncle Adamu, ta yaya za mu dakatar da waɗannan ƙudajen? Ba za mu iya rufe banɗakunan ba, makaranta tana buƙatarsu.

**ADAMU** Za mu iya bai wa makarantar shawara game da hanyoyin da za su riƙa kula da banɗakunansu.

**SAMA'ILA** Ta yaya za a iya lura da wuraren ba-haya?

**ADAMU** To dai da farko, dole ne a riƙa tsaftace banɗakunan fiye da sau ɗaya a kowace rana. Dole kuma mutanen da suke yin aikin, su sanya safar hannu domin kariya.

**HADIZA** To! Idan kuma babu ruwa fa? Ba a ko da yaushe ba ne ake samun ruwa a makaranta.

**ADAMU** Makarantu masu yawa ba su samun ruwa a ko da yaushe. Idan haka ne, dole ne ku samu toka ku riƙa baza ta a kan daɓen banɗakunan.

**SAMA'ILA** Toka? Toka dai da ake samu daga wuta? Toka? Wannan ya sake tunatar da ni abincin ayaba haɗe ta toka wanda Anti Mariya, babar Hadiza, ta so ta ciyar da ni, lokacin da nake rashin lafiya. Ka tabbata?

**ADAMU** Ai Sama'ila, da ka ci wannan abincin, da bai taimaka maka ba. Amma a wannan karon, toka za ta taimaka maka sosai.

Ku duba, yawancin waɗannan banɗakunan ba a yi musu daɓen sumunti ba. Ya kamata a riƙa wanke waɗanda ke da sumunti da ruwa a kai-a kai.

**HADIZA** Da kuma waɗanda ba su da sumuntin?

**ADAMU** A nan batun toka ya shigo. Ku yayyafa ta a kan daɓen sumuntin da daddare, sannan ku fara wanke wurin tun da sassafe.

**SAMA'ILA** Ni fa har yanzu ban fahimta ba. Saboda mene ne za a yi amfani da toka?

**ADAMU** Wasu 'yan ƙananan zare-zare da ke cikin toka, su ne sukan hana wasu 'yan tsutsotsi ƙanana yin numfashi, wanda hakan zai rage adadin ƙudaje a wuri. Amma kuma dole ne a kawad da su kafin a yi amfani da banɗakin. Domin idan tokar ta gauraya da fitsari za ta iya taimakawa ƙwayoyin cutar su yaɗu! Don haka ne, dole mu yi hattara.

**HADIZA** Ka ce mu riƙa wanke daɓen sumuntin. Amma yawancin lokuta ba mu da isasshen ruwa.

**ADAMU** Ina ba da shawara cewa, kowane ɗalibi ya kawo wata ƙaramar kwalbar ruwa. Da wannan ruwan, za ku iya wanke daɓen da dogayen tsintsiya da kuma maƙata mai haɗe da tsumma da za a riƙa busar da wurin.

**HADIZA** Maƙata mai haɗe da tsumma?

**ADAMU** E, amma kuma ba za a matse ta ko juya wannan tsumma da hannu ba! Wani abu kuma shi ne, dole a riƙa rufe ƙofar ramin wurin yin bayan-gida idan an gama amfani da shi.

**SAMA'ILA** Shin Kawu, ta yaya mutum zai rufe ƙofar?

**ADAMU** Za mu iya buƙatar hukumar makaranta ta samar da marafai waɗanda za a ɗaura wa dogayen sanduna da za a riƙe idan za a rufe ramin yin bayan-gidan. Suna da sauƙin yi da kuma araha.

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | Wayyo! Kawu Adamu, akwai abubuwa masu yawa da suka kamata mutum ya koya. |
| **HADIZA** | Kaina yana bugawa saboda waɗannan bayanan da muke samu. |
| **ADAMU** | Da ma za a yi tsammanin haka. Amma kuma waɗannan ayyuka ne masu sauƙi, waɗanda za mu iya yi a ko da yaushe a lokacin rayuwa. Yanzu bari mu je mu yi magana da hukumar makaranta. |
| **HADIZA** | Ya yi! Sai mu bi ta nan ko? |
| **ADAMU** | Kai! Amma mun manta da wani abu guda mai muhimmanci. |
| **SAMA'ILA** | Wannan wane abu ne kuwa? |
| **ADAMU** | Wani wuri kusa da banɗaki inda ɗalibai za su riƙa wanke hannuwansu da sabulu bayan sun yi amfani da banɗakin. A wurin da babu ruwan famfo, hukumar makaranta za ta iya samar da wani duro wanda za a maƙalawa a kan famfo. Za kuma a iya yin amfani da garewanin da aka huda, a wuraren da babu duro ko tanki mai kan famfo. |
| **HADIZA** | Garewani masu yoyo? |
| **ADAMU** | E, kamar a yi wata 'yar huda daga ƙasan duro ɗin. Za a iya maƙale wannan a jikin wata itaciya ko saman dakali kusa da banɗakunan. |
| **SAMA'ILA** | Amma kuma, ai duk ruwan zai zube. |
| **ADAMU** | Tunani mai kyau! Za ka iya yin amfani da wani abin da zai dakatar da ruwan wanda za a ɗaura a jikin wata 'yar sanda da za a riƙa kulle ruwan da shi, idan yana tsiyayewa. Abin da ake so mutum ya yi a nan shi ne, ya riƙa cire maƙatar da aka ɗaura wa abin tsayar da ruwan, ya wanke ta da hannu, sannan ya mayar da ita. |
| **HADIZA** | Abin gwanin ban sha'awa. Daga nan duk sai mu yi waƙar wanke hannuwa. |

**HADIZA da SAMA'ILA**

*Ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku*
*a yayin cin abinci.*
*...*

**MAI GABATARWA**

Na san wasu masu saurare za su yi mamakin jin yadda yin aiki da wasu hanyoyi masu sauƙi zai iya taimakawa a nisanci wasu hatsuran da ke yin barazana ga lafiyarmu, muddin muka sanya su cikin ayyukanmu na yau da kullum. Ta ɗaya gefen kuma, a sanadiyyar ayyukan da Sama'ila da Hadiza suke yi tare sai haɓaka yake yi, domin kuwa abota ce mai muhimmanci wadda za ta taimaka wa sauran jama'a. Ta dalilinsu sannu a hankali, za a iya kyautata kiwon lafiya sosai a makaranta da kuma a gida. Yayin da suke ci gaba da sa himma, wane wuri ne kuma Sama'ila da Hadiza za su kai mu nan gaba?

A kasance da mu a shiri na gaba domin ɗorewar wannan shirin. Kafin nan ana iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw.world.de/lbe, domin sake sauraron wannan shiri ko kuma aiko da tsokaci.